
# FADAKARWA

## A kan: Kasuwanci da tallace-tallace

## <u>Kashi na 4:</u> Tafarkin inganci kaya

### Fahimtar tafarkin ingancin kaya?

Idan a na so ingancin amfanin gona ya dore, dole ne duk masu harkar kayan noma, kamar masu shigo wa dasu cikin kasa, masu sari domin sayar wa, kananan yan kasuwa, manoma, hukumomi da kuma jama'a masu sayen kayan abinci su hada kai da kuma tabbatarwa kowanne ya yi abin da ya kamata a matakinsa.



Sabo da haka, harkar wadata jama'a da abinci al'amari ne da ya shafi bangarori da yawa, daga kamfanonin da suke samar da kayan noma har zuwa manoma kamar yadda a ka yi bayani.

Amma duk da cewar da yawa daga kayan noman da a ke amfani da su a Nigeria a na shigo wa da su ne daga kasashen ketare, akwai wasu manyan kamfanoni da suke samar da kayan noma a cikin gida, misali akwai kamfanin Notore a Port Harcourt wanda yake samar da takin NPK da kuma kamfanin Federal Superphosphate Fertilizer da  ke Kaduna wanda shi kuma ya ke yin takin Single Superphosphate. Sa'annan akwai kamfanoni irin su Premier Seeds da Alheri Seeds na Zaria wadanda suke samar da ingantattun irin shuka.

## How is value added?

Za a iya takaice matakai daki daki a tsarin kasuwanci daga kamfanin da yayi kaya har zuwa mai amfanin da kayanm, kamar haka

- Kamfanin day a yi kaya.
- Babban dan kasuwa mai sayo wa daga kamfani(gida ko kasashen waje).
- Wani babban dan kasuwa mai saye da yawa domin sayarwa day an sari.
- Matsakaitan yan kasuwa masu saye sari domin sayarwa da kananan yan kasuwa.
- Kananan yan kasuwa wadanda zasu sayarwa jama'a masu amfani da kaya.
- Jama'a masu sayen kaya domin amfani da su.

A kowanne daga cikin wadannan matakan kasuwanci, kaya suna kara samun daraja, kamar haka

- Kamfanonin yin kaya suna sarrafa kaya.
- Manyan yan kasuwa sauna shigo da kaya ciikin kasa.
- Yan sari suna sufurin kaya zuwa cikin kasa.
- Kananan yan kasuwa suna sufurin kaya zuwa kauyuka da yankunan karkara donim sayarwa jama'a.
- Sauran masu ruwa da tsaki a wannan …… kamar hukumomi, masu sufure da bankuma suma suna bayarda gudummawa kala kala wajen taimakawa kamfanoni da yan kasuwa.